# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da



# Babban Bango na Nehemiya

**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Jonathan Hay**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Mary-Anne S.**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**

**Farsiya, al’umma mai iko, ta yi mulkin duniya. Sarki Artazezes ya yi mulkin Farsiya. Wannan ya mai da shi mai mulki mafi karfi. Wani mutum mai muhimminci mataimaki sarki Bayahude ne mai suna Nehemiya. Aikinsa shi ne ya taba abincin sarki don ya tsare abincin daga guba.**



**Wata rana, Nehemiya ya zo gaban sarki da fuskar bakin ciki. Sarki ya so ya san mene ne damuwan. "Ya sarki, ranka shi dadde," Nehemiya ya ce. "Ina bakin ciki saboda birnin da aka binne kakannina yana a rushe kuma kofofin shiga birnin an kokkone." Nehemiya yana magana game da Urushalima ne, wanda aka halakar ta wurin yaki shekaru da dama da suka wuce.**



**Sarki Artazezes ya tambaya, “Mene ne kake so?” “Bari in tafi Urushalima domin in sake gina ta,” nehemiya ya roka. Sarki Artazezez cikin kirki ya yarda. Ya kuma ba wa Nehemiya wasika na musamman don ya tsare shi yayinda yake tafiya.**



Sarki ya kuma taimaka fiye da.  Ya ba wa Nehemiya wasika zuwa wurin Asaf, mai lura da kurmin sarki.  An ba wa Asaf oda ya ba wa Nehemiya duk yawan katakon da yake bukata domin gina bangon birnin.



Sa’ad da Nehmiya ya kai Urushalima, ya tattara shugabannin birnin ya ce, “Muna a cikin matsalla a nan.  Birnin yana a rushe kuma kofofin shiga garin an kokkone.  Bari mu fara giggina su kuma.”  Ya gaya musu Sarki Artazezesya ba da yardarsa, abu mafi muhimminci shi ne, Allah yana tare da su.



**Irin bangaskiyar Nehemiya da kwazonsa ya sa mutane suka ta da zukaatansu ga aikin. Suka yarda, suna cewa, "Bari mu sake gina wa." Nehemiya ya gaya wa kowane iyali gefen bangon da za su gyara.**



**Amma, ba kowa ba ne ya yarda a sake gina bangon birnin. Wani mutum mai suna Sanballat, da abokansa biyu Tobiya da Geshem, su ba Yahudawa ba kuma ba su so a sake gina bangon ko a**



**gyara kofofin shiga garin ba.**

Yayinda aikin na ci gaba, Sanbalat ya fara fushi sosai. Da shi da abokansa sun fara yi wa Yahudawa gori. Tobiya ya ce, “Bayan da sun gama gina wannan bangon kara, dan karami kurenge zai rushe shi har kasa.” Nehemiya bai tanka su ba. Maimako, ya yi addu’a don Allah ya yi musu hukunci.



**Sa’ad da zagin gorinsu bai yi tatsiri ba, sai suka fara kulle-kulle su yi fada da Urushalima don kawo damuwa da rikicewa daidai yadda za su iya. Kuma, Nehemiya ya sake yi addu’a ga Allah don neman taimako. Ya kuma sa maigadi dare da rana don kada su dauke su babu shiri.**



**Yahudawa suka yi aiki cikin kwazo, sun fara gajiya.  Wadansu sun fara jin tsoro cewa abokan gab za su iya kawo musu hari su kashe su yayinda suke cikin aiki.**



Nehemiya yi kokari ya zama abin koyi garesu. Sarki Artazezes ya riga ya mai da shi

Gwamna a Urushalima da ‘yancin ya sa mutane su kawo masa abinci da kudi, amma bai yi haka ba. Shi dai ya yi aiki da kwazo tare da mutanen yayinda suke sake gina bangon. Ya yi amfani da kudinsa yana saya abinci.



**A karshe, mutanen suka gama gina bangon, sai kofofin ne sun rage a sa bakin kofofin shiga birnin. Bayan da Sanballat, Tobiya, da Geshem suka ji cewa ko’ina an rufe a bangon, sai suka shirya su ji wa Nehemiya mugun abu.**



**Sai suka aika sakonni wa Nehemiya domin ya sadu da su a wani wuri mai suna Ono. Amma Nehemiya ya san shirinsu don suna so ya fita daga cikin birnin ne don ji masa rauni. Sai shi ma ya rubuta musu cewa ba zai bar aikin da yake yi ba don ya ziyarce su.**



A karshe an
gama bangon,



sai Nehemiya ya
sa ‘yan tsaro domin
su tsare shi.



Ya yi wani doka kuma cewa ba za a bude kofofi bas

ai bayan rana ya fito sosai.  A cikin dare, za a rufe su a kulle su.

Yanzu birnin yana nan lafiya, yawancin Yahudawan da suke kasar bauta a wurare dabam-dabam a ko’ina a duniya suka dawo Urushalima. Nehemiya lallai kam ya yi farin ciki sosai cewa ya kamala aikin da Allah ya ba shi ya yi, duk da matsallolin da ya samu. Ya zauna a Urushalima ya taimake mutanen su yi wa Allah biyayya kullum.



# Babban Bango na Nehemiya

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Nehemiya**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

35

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**